UNHCR
The UN Refugee Agency

PRACTICAL SHEET

# TAMBAYOYI GOMA (10) DA ZA'A AMSA KAFIN KADDAMAR DA KAMFEN NA SADARWA TA SAKON WAYA

**SHIN ZAKA SO KAFA WANI HANYAR SADARWA TA SAKON WAYA DON MUSAYA BAYANI DA AL'UMMOMI? GA WASU SHAWARWARI DON JAGORA A LOKACIN SHIRYA TSARIN.**



## 1. SHIN TURA SAKON WAYA WANI HANYA NE DA YA 'DACE'?

- Shin anyi wani binciken bayanin da buƙatun sadarwa na al'ummomin, don sanin idan sakon waya na daga cikin hanyoyin da suke amfani dashi (ko kuma zasu so amfani)?
- Shin rukunai jama'a da kuke so ku sadar dasu na samun isasshen damar wayoyin hannu?
- Idan ba'a ambaci sakonnin waya ko wasu mutane ne kawai ke amfani dashi, kamfen naka ta sakon waya bazai yi tasiri yadda ake so.



## 2. ZA'A IYA MAIDA AMSA GA SAKON KA?

- Koda kuna so ku amfani da sakon waya kawai don wallafa bayanai (ba'a buƙatar amsa), wata kila mutane zasu iya jin buƙatar maida muku amsa.
- Koda kun rubuta "KADA A AMSA", duk da haka sai an samu sakonni masu shigowa.
- Don gujin barin sakonni na gaggawa ba tare da maida amsa ba, shirya wani tsari don amsa sakonni masu shigowa yadda ya dace.



## 3. SHIN KUNA DA ISASSHEN KAYAYYAKI?

- Bincika naku ƙarfin na cikin gida wajen tsara, bada, da lura da wannan hanyar (gudanar da ɓangaren fasaha, rubuta sakonni ...)
- Kafin farawa, tabbatar tare da abokanai aiki da abun ya shafa idan suna da lokacin shigar wannan tsarin.
- Idan baka da isasshen kaya, wata kila zai fi in ka samu wani mai bada tsarin daga waje wanda zai iya rage maka aikin.

**PRACTICAL SHEET**



## 4. SHIN KA SHIRYA DABARUN KA?

- Dabarun yana nuna cikakken tsarin aikin ka mataki bayan mataki. Yana bayyana wanene ke da alhakin kowane aiki da yaushe.
- Dabarun ka zai tantance wace ƙungiya ne yafi dacewa idan za'a ɗauke mataki sakamakon sakon da aka samu.
- Wannan zai guji haɗarin cewa ba za'a magance wasu buƙatu na gaggawa.



## 5. WAƊANSU KAYAN AIKI ZA'AYI AIKI DASHI?

- Tura sakonni wata kila zai buƙaci amfani da wasu fasaha.
- Wata kila zaka buƙaci wani tsari wanda zai jera sakonnin gaggawa akan matsaloli na musamma (kamar GBV).
- A dabarun ka, bayyana dukkan kayan aiki wanda dole ne kayi amfani dashi don gujin abubuwan ban mamaki da ba'a shiryawa ba.



## 6. SHIN AN WARE WANI?

- A wani al'umma, ba kowa yake samun dama iri daya zuwa wayar hannu (mata, tsofaffi, da sauransu). Yi tunani game da yadda za'a hada da dukkan rukunai jama'a a sadarwar ka.
- Misali, ta shigar da tsarurrukan al'umma don wallafa bayanai ta maganar baki zuwa rukunai jama'ar da basa samun damar wayar hannu.
- Wata kila za'a buƙaci raba na'urori don wasu rukunai jama'a.



## 7. SHIN AN RIGA AN FARA AMFANI DA SAKON WAYA A WANI WAJE?

- Kungiyoyi da yawa na iya amfani da sakon waya a lokaci ɗaya. Dole ƙungiyoyin agaji su daidaita kuma su haɗa kai saboda kar su tsoratar da al'ummomi da sakonni.
- Misali, shirya wani ƙungiyar masu aiki akan sadarwa tare da al'ummomi, da hada kai ƙungiyoyi da dama.

**PRACTICAL SHEET**

## 8. YADDA ZA'A AUNA TASIRIN SAKONNIN WAYA?

- Kafin tura dubbai sakonni, gwada bayanin ka da wasu mutanen garin tukunna don tabbatar fahimtar sakon ka da kuma shiryawa kuskuren fassara mai yiwuwa.

## 9. NAWA NE FARASHIN?

- Don gano farashin, tantance yawan mutanen da kake so ka isar musu da sakon, yawan sakonnin da kake so ka tura, da farashin ma kowane sako.

- Tuntubi kamfanoni masu bada sabis don tattauna akan farashi da zai fi.

## 10. KANA BUKATAR WANI MASLAHA NA CIKIN GIDA?

- Kafin zuba babban hannun jari, gwada tsarurruka daban-daban da kuma kamfanoni masu bada sabis daban-daban. Wannan zai fi baka tunani akan wani irin maslaha kake buƙata.

- Misali, zaka iya gwada wani kamfani mai bada sabis na “ɗan wani lokaci”. Wannan zai taimaka maka da cire zaɓin da basu dace da buƙatun ka ba.

- Bayan waɗannan gwajin, zaka sani idan kana buƙatar wani maslaha na shiryawa da kanka (DIY) ko ka bi ta wani daga waje.



More tools and tips
on communicating with communities are available on the website:
cwc.westafrica.exposed